# Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin ƙai.
# Mene ne Alkur'ani Mai girma?

Alkur'ani mai girma shi ne zancen Allah Ubangijin talikai kuma mahaliccinsu, Ya saukar da shi ga cikamakin Annabawa da Manzanni Annabi Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - don ya bayyana wa mutane manufar halittarsu, da kuma shiryar da su zuwa ga abin da akwai tsiransu a cikinsa a duniya da lahira, da kuma tsamosu daga taɓewa ta har abada bayan mutuwa, shi ne karshen sauka a littattafan Allah, mai gasgatawa garesu, kuma mai shafewa ga shari'unsu.
Alkur'ani Mai girma aya ne kuma mu'ujiza ce ta har abada, kuma shi dalili ne a kan Annabcin Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -, Allah ya yi wa muatne da aljanu fito-na-fito a kan su zo da kwatankwacinsa kai ko da sura ce daga gare shi, sai suka gajiya daga hakan.
Canji bai taɓa shi ba tun saukarsa kafin sama da shekara 1400, kuma zai wanzu abin kiyayewa da harshen Larabcin da ya sauka da shi, yayin da Allah Ya dauki lamunin kiyaye shi har zuwa karshen zamani.
Alkur'ani Mai girma shi ne tushe na asali ga musulunci, kuma shari'ar da take tsara rayuwar ɗan Adam kuma ya ke hukuntata a kowanne zamani da wuri, yana kira zuwa bautar Ubangiji Mahalicci Shi kadai, kuma yana bayyana abin da mutum yake bukatarsa don sanin Ubangijinsa da Addininsa, kuma farkon halittar kasantacce, da matakan halittar mutum, kuma yana ba da labari na gaibobi waɗanda suka wuce da masu zuwa, da labaran Annabawan da suka gabata - aminci ya tabbata a gare su -, kuma ta yaya Allah Ya ba su nasara ya kuma halakar da makiyansu, a cikinsa akwai tushen ibadu da mu'amaloli da kira zuwa kyawawan dabi'u, da gargaɗarwa daga dabi'iu ababen zargi, da makoma a lahira; ko dai a Aljanna gidan muminai ko kuma wuta gidan azzalumai da kafirai.
Sabo da muhimmancin wannan littafin Mai girma, wanda Allah Ya saukar da shi da harshen Larabci, kuma Ya yi umarni da isar da shi ga 'yan Adam; yana faranta mana rai - ya kai mai karatu mai girma - muna gabatar maka da fassarar ma'anoninsa da harshenka, don saukakawa ga fahimtarsa, da kuma tabbatarwa ga isar da shi, hakika wadanda suka yi wannan aiki, sun yi iya kokarinsu a cikin fahimtar ma'anoninsa da fassararsa, tare da ilimi na sakankancewa cewa shi duk yadda zurfin fassara ta kai za ta gushe abar takaituwa daga ba da ma'anoni masu girman da nassosin Alkur'ani mai girma su ke nuni a kansu, mai gajiyarwa wanda ya ke zarce kowanne aiki na dan Adam, wanda yake son ya tsaya a kan kari daga hakikanin da Alkur'ani mai girma ya zo da su; to, muna yi masa wasici da ya koyi harshen larabcin da ya sauka da shi.
Aminci ya tabbata ga Manzanni, godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

Mau'su'ah ta Akur'ani Mai girma (Bakandamiar Alkur'ani Mai girma)
www.quranenc.com

Yana faranta mana rai mu karɓi shawarwarinku da gyararrakinku don ci gaban fassarar ta hanyar kafar gyararraki wadda ta ke a gaban kowacce aya a shafin mau'su'ar Alkur'ani Mai girma (www.quranenc.com), kuma inda sha'awar tuntuɓarmu zai yi wu a yo mana aike ta hanyar shafin yanar gizo: info@quranenc.com

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin ƙai.
Mene ne Alkur'ani Mai girma?